Citation: Fallou Ngom (PI), Jennifer Yanco, Mustapha Hashim Kurfi, Garba Zakari, Babacar Dieng, Daivi Rodima-Taylor, and Rebecca Shereikis. 2022. "The Harlot's Song." http://sites.bu.edu/nehajami/the-four-languages/hausa/hausa-manuscripts/falke-1486-wakar-karuwa/.

# **Waƙar Karuwa**

Bismi l-Lāhi al-Raḥmāni al-Raḥīm, ṣallallahu ʿalā l-Nabiyyi l-Karīmi

Waƙar Karuwa, Uwar Mugu daga Hamisu Yadudu Funtua

Allāh sarki da yai mu duka Ka yafe dhanbbanmu dan rahmarka

Ka tsarasshemu daga aiyukan halaka Muna yin yabo da salati duka

Ga Annabi Shugaban Rai duka

A ya ƴan uwana samari ku zo Ku dubi abinda yake je ya zo

Ku dena haƙilo a hanga hazo Kar dai ka yarda da shiftar gizo

Nufi na kilaki uwar masu cizo

Karuwa ba ta gwani ku fahimta Kowa ya bata, shi ne gwaninta

Buƙatarta safe da yamma a bata Kowa ya ɗaukewa ɗauka buƙata

Watan wataran za shi koma baranta

Kar ka bi hanyarta ɓata gari Kar ka bi don ba ta kai ka gari

San dai ta kai ka takin hadari A maishe ka wawa kana garari

A ƙarshe ta barka da roƙon ɗari

[Page 2]

Takan yadda malam da hila tata Dalilinta sarki yakan bar sarauta

Takan maida tajiri, ɗan farauta Takan kashe aure da gulma tata

Kowa bi hanyarta ya bi ɓata

Malam tsaya ka ji halin kilaki    Na farkonsu dai ba ruwanta da aiki

Babbar iyadarta wanka da wanki    Idan ta ce ta ƙoshi mai share ɗaki,

Ta hau kan kujera ta koma a ɗaki

Takan sake murya idan ta ga kurɗi    Ta ce ita Ikko take ko Makurɗi

Idan ta ji sunanka ba ta faɗi    Takan zaɓi suna da duk ya fi daɗi

Ta sa maka domin ta samu kuɗi

In ta ga ta harbu, ba ta faɗi,    Sai tai shiru kowa fa na baya faɗi

Ke ƙoƙi ko uwar ƙin kaɗi    Halinta ƙarya da zamba da ruɗi

Algunguma mai idan cin kuɗi

Tana maida zance tana rangwaɗa    Tai magana sai ka ce mai raɗa

Tana yi tana ɗaga ƴan kafaɗa    Kamar wanda ya shiga filin kiɗa

Ka ji ƙarautau maras mafaɗi

[Page 3]

In ko ta ganka da halin talauci,    Sai ka ga ta murtuke don butulci,

Takan tsiri shara tana feshe hanci    Koko ta ce tashi ni zan yi barci

Dan ta ga ba ka da kaya na ci

Akwai sake suna wajen karuwa    Idan ka ji sunanta Kande a Yarwa

A birnin Kano ka ji sunanta Yalwa    Koko ta ce Binta mai aduwa

Sunanta ya fi dubu karuwa

Sunanta A'i cikin Katsina    A Sokoto ko sai ta ce Maimuna

Ko kuwa Rabi idan tai Kaduna    Sunanta Ladi a birnin Mina

Na Ikko daban ne da na ko'ina

Aboki kazan yi kana Ankarra    Cutarta ta fi gaban gobara

Haskenta ba **arziqi** sai Khasara    Sanyi a gindinta ya fi kwara

Ka lura, ka saurari tau shawara

Takan tsiri yawo da babu dalili    Takan guzurin maida ɗan goro, ƙyalle

Madubi da hoda kamar za ta koli    Takan kwalliya ta fito dandali

Babban zagi nata shi ne kawali

[Page 4]

Būrinta sabon gari ko fagge    Yawanci tudun wada can suka dage

Da su da maroƙansu fuska su goge    Molo, garaya suke so da goge

Kaɗan karuwai babu tankar ya goge

Giya ce abincinta safe da yamma    Ba ta buƙatar tuwo ko rama

Wai ita ta riƙa sai alkama    Sai alkubus wata sa'a da nama

Ruwan shanta ma sai takan sa zuma

Takan ƙin rakaka da kayan ado Fulloli, katifu ta ɗaura gado

Ta sa tangaran masu ɗaukar ido Idan za ta yawo ta kanne ido

Da ta dawo yawo sai ta koma gado

Ba karabata da ƙamshin turare Takan sanya zoben azurfa fari

Takalmanta ja-ja irin na baturai Da ɗan Ashoke tana goge haure

Baƙinta ba su zuwa sai dare

[Page 5]

Auranta bai fin watanni shidda Ko ta kasha ba ruwanta da Iddah

Inna wadda ta auri soja shidda Ki koka idan sunka komo gida

Rannan kare za shi kama gada

Ko me kake bata ba ta da so Cikin sha'ani nata sai yarda ta so

Kar kaga ta nuna kai ɗin take so Akwai ku da dama da ta ce tana so

Takan ƙi ƙido takona ake so

Laifinta ɗai da maneni nata Kowa yace gafiya na da sata,

Kusan daudawa ma fa wari gareta Babu rabewa da yalo da ɗata

Masaƙar gudu nai ake saƙa sata

Ɗan daudu wawa maras mafaɗi Katuba ga Allah kabar maguɗi

Shine fa kanwa uwar ƴan haɗi Kabar ɗaura gyauto kabar yafa shuɗi

Kazan sanya riga kana yin naɗi

[Page 6]

Kowa ya yarda da su ya yi kūka — Da su da abokansu ƴaƴa na iska

Idan ka ga tāronsu kauche abinka — Ko sun kirawo ka ma kar ka tanka

Idan ka ƙi jin shawarata ruwanka

Alḥamdu li l-Lāhi na ƙare waƙa — A wannan wurin ne na kai matuƙa

Khāmisu Yādūdu yai wagga waƙa — Kar kuga baida fusāḥā ga waƙa

Ku dai ku dubi nufi ba nifāqa

To jama'a kun ji nawa kalami — Ku san yadda za ku yi ku ƙetare rami

Dabara ku san ba ta ɗaure dami — Kayan aras ba a ɗorawa gomi

Kare da biri ba su jure gami

Tammat bi ḥamdi l-Lāhi

Ismi l-kātib Muḥammadu

Ɗan Gurgu, Kano-Darma,

Nigeria

Bi salāmi